# Haɗa kai da matasa/ƙungiyoyin matasa domin ƙwanƙwance ƙarfi da rauni

Wannan takardar aiki tana ɗauke da jerin tambayoyi da za a iya amfani da su yayin tattaunawa da matasa. An tsara waɗannan tambayoyi ta yadda za a tattauna da matasa game da yadda suke mu'amala da al'ummarsu, gano waɗansu abubuwan da za su iya taimaka wa lamarin tsattsauran ra'ayi, tare kuma da gano damarmakin da ake da su domin jawo hankalin matasa ta yadda za a kauye wa VE.

**TAMBAYOYIN JAWO HANKALI: Waɗannan tambayoyi na farko sun kasance na janyo hankali tare da taimakawa wajen gabatar da batutuwan da za a tattauna zuwa ga mahalarta ta yadda mahalartar za su saki jiki da wurin**

- Mutane nawa ne daga cikinku suke cikin wani al'amarin da ya shafi bunkasa al'umma?
- Waɗanne al'amura ne kuke saka kanku ciki a cikin al'ummarku?
- Waɗanne dalilai ne ke sa ku saka kanku cikin al'amuran sannan waɗanne dalilai ne ke sa kuke biris da su?

**TAMBAYOYIN NAZARI: Waɗannan tambayoyi an tsara su ne domin fahimtar buruka, ƙarfin guiwa, da ƙalubale**

- Yi bayanin wani game da wani da ya yi nasarar rayuwa a cikin al'ummar nan sannan ku yi bayanin dalilin da ya sa kuka ɗauki mutumin a matsayin mai nasara?
- Waɗanne damarmaki ne ake da su amma waɗanda ba za ku iya kaiwa gare su ba? Mene ne dalilan?
- Wane nau'in ƙwarewa/ilimi ne matasa ke da buƙatar samu domin su iya magance matsalolinsu da matsalolin al'umma?
- (Misali, ƙwarewa a fannin sadarwa, jagorancin shiri, shawo kan rikici, sarrafa kayan aiki, samar da mafita ga matsala, haɗa kan al'umma, fasahar zance, bunkasa shugabancin matasa)
- Waɗanne nau'ukan keɓantattun bukatu ne ke da wahalar cimmawa a cikin al'ummarku?
- Waɗanne zabuka marasa kyau ne kake tunanin matasan da ka sani za su iya yi yayin da ya kasance zabuka sun yi ƙaranci?
- Me ke sa matasa su yanke hukuncin aiwatar da ayyuka masu haɗari?
- Waɗanne abubuwa ne ƙungiyoyi da mahukunta za su iya yi domin taimaka wa matasan al'ummarku domin samun ci gaba?
- Ta waɗanne hanyoyi ne matasa za su iya taimakawa domin inganta rayuwa a cikin al'ummarku?
- Shin akwai wani abu na daban wanda za ka so ka bayyana game da halin da matasa suke ciki a cikin al'ummarku?